Meke damun wasu mutane ne suke ɗaga idanuwansu zuwa sama a cikin sallarsu". Sai maganrasa ta yi tsanani a kan hakan, har ya ce: "Kodai su hanu daga hakan ko a fauce magannansu

Daga Anas ɗan Malik - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Meke damun wasu mutane ne suke ɗaga idanuwansu zuwa sama a cikin sallarsu". Sai maganrasa ta yi tsanani a kan hakan, har ya ce: "Kodai su hanu daga hakan ko a fauce magannansu".

[Ingantacce ne] [Bukhari ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya gargaɗi waɗanda suke ɗaga idanuwansu zuwa sama a cikin sallah a lokacin addu'a ko waninta, sannan tsawatarwarsa ta yi tsanani da narkonsa - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - akan wanda ya aikata haka da cewa shi yana jin tsoro akan idanuwansu kada a fauce musu su a karɓesu da gaggawa ta inda basa ji sai kawai ga shi sun rasa n'imar gani.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/10883